
# Kwaɗo Ya Tafi Birni



Mustafa Kalkal
Mai Fassara


# Kwaɗo Ya Tafi Birni



Published by:
STELLAR (STudents Empowered through Language, Literacy, and ARithmetic)
American University of Nigeria
Lamido Zubairu Way, Yola By-Pass
Yola, Adamawa State, Nigeria PMB 2250
http://www.americanuniversitynigeria.org

This book is an adaptation and translation from English to Hausa of the shell book *Froggie Goes to Towan* by Cathy Krekel, illustrated by Jeff Whetstone © 1992 SIL-PNG.

**Kwaɗo Ya Tafi Birni (Hausa)**
© 2013 American University of Nigeria / CC-BY-NC-3.0
Permission is granted to download, copy, adapt, translate, and/or distribute this book in any media, for noncommercial purposes, with attribution to the original author(s), translator(s), illustrator(s), publisher, and funder(s), where applicable, under the terms of the Creative Commons Attribution NonCommercial 3.0 Unported License. Electronic copies of this and other books are available for free at:
www.americanuniversitynigeria.org/about/dev/stellar



Wata rana Kwaɗon ƙauye da
abokinsa suna shan rana,
sannan wani sabon tunani
ya zo ma Kwaɗo.

Kwaɗo ya ce, “Na
ji akwai manyan ƙudaje a
birni.  Ina ga ya kamata in
tafi birni.”

Sai abokinsa ya ce, “Amma
yaya za ka yi ka tafi birni?”
Kwaɗo ya amsa, “Zan yi
tsalle a kan tifa ta kai ni
birni.”

Sannan sai ya tashi ya je neman tifa. Nan take sai ya ga tifa tana wucewa a kan hanya. Sai Kwaɗo ya yi tsalle, amma ya yi tsalle sama sosai ya wuce kan tifar. Haka ta wuce ta tafi ba tare da Kwaɗo ba.

“Yanzu yaya za ka yi ka tafi birni?” abokinsa ya tambaye shi.

Sai ya amsa, “Zan ɓuya cikin jakar mutumin nan idan ya tashi tafiyar birni ya tafi da ni.”

Amma washegarin da mutumin ya tashi tafiyar birni sai ya manta da jakarsa. Haka ya tafi ba tare da Kwaɗo ba.

“Yanzu yaya za ka yi ka tafi birni?” abokinsa ya tambaye shi.

“Zan tafi a cikin buhun shinkafa idan za a tafi kasuwa da shi,” Kwaɗo ya amsa.

Sannan ya tashi ya shiga wani buhu ya ɓuya. Amma mota ta cika da buhuhuna babu wajen sa wadansu. Haka ta tafi ba tare da Kwaɗo ba.
“Yanzu yaya za ka yi ka tafi birni?” abokinsa ya tambaye shi.

“Zan tafi a kan bayan tsuntsu,” Kwaɗo ya amsa. Sannan ya tafi neman tsuntsu.  Tsuntsu ya tashi da Kwaɗo har iska ya hure Kwaɗo ya faɗo a ƙasa.

Haka tsuntsu ya tafi ba tare da Kwaɗo ba.

“Yanzu yaya za ka yi ka tafi birni?” abokinsa ya tambaye shi.

“Zan tafi birni da kaina yanzu kam,” Kwaɗo ya mayar masa. Sannan ya tashi ya kama hanyar birni da tsalle.

Kwaɗo yana ta tsalle a hanyar birni ...

yana ta tsalle ...
yana ta tsalle ...

… har sai da Kwaɗo ya isa birni.

Sai ya sadu da Kwaɗon birni, ya tambaye shi, “Ina kwana? Don Allah, ina manyan ƙudajen birni masu jiki?”

Kwaɗon birni ya amsa,
“Manyan ƙudajen birni?  Ai, babu manyan ƙudaje masu jiki a birni.”
“Muna da ƙananan ƙudaje ne kawai.  Dukan manyan ƙudaje suna  ƙauye!”

Sai Kwaɗon birni ya yi tsalle ya koma gidansa, ya bar Kwaɗo ƙauye.


Kwaɗo abin tausayi, bai da abun yi kuma sai dai ya koma gida a ƙauye.

Da Kwaɗo ya dawo daga birni, ya sami abokinsa.

Abokinsa ya tambaye shi, “Yaya batun manyan ƙudajen birni?”

Kwaɗo ya ce, “Ka gane ba, abubuwa ba su fi kyau a wasu wurare ba kamar yadda muke tsammani.”

Sannan suka ci gaba da shan ranarsu a kogi.



## Tambayoyi

1. Me ya sa Kwaɗo ya tafi birni?
2. Yaya Kwaɗo ya fara farkon ƙoƙarin tafiyarsa a birni?
3. Me ya faru a lokacin da Kwaɗo ya tashi a kan bayan tsuntsu?
4. Yaya Kwaɗo ya yi ya tafi birni a ƙarshe?
5. Me Kwaɗo ya koya a cikin labarin?

Bayani Ga Iyaye:
Sau da yawa bincike ya nuna cewa koyon karatu a harshen da yara suka saba, watau harshensu, na garinsu, ko na al'ummarsu, yana taimako sosai wajen ƙara masu saurin koyo da kaifin fahimta. Mafi yawan yara da suka fara karatu da harshensu suna fin sa'o'insu da ba su fara da harshensu ba a karatun wani harshe. Misali, idan yara masu jin hausa sun fara karatu da hausa, karatun hausa zai taimaka sosai wajen koyon karatun turanci. Haka kuma yara za su fi fahimtar kalmomi da ma'anarsu na sabon harshe idan sun sami matashiya a nasu harshen. Matakin da ya fi dacewa ku ɗauka na inganta karatun yaranku shi ne ku kwaɗaita masu karatu kullum a harshensu kafin su fara koyon turanci, kuma su ci gaba da karatu.